# YADDA YA KAMATA A FAHIMCI DOKAR 'YANCIN SAMUN BAYANAI (FOIA) TA 2011

## MUHIMMAN AL'AMURA 10 DA DOKAR FOIA TA SHEKARAR 2011 TA TABO

## DA

## AL'AMURA 10 MASU RIKITARWA GAME DA DOKAR FOIA TA SHEKARAR 2011

**Wallafar**

R2K RIGHT TO KNOW ....YOUR LIFE DEPENDS ON IT

Da taimakon

OPEN SOCIETY INITIATIVE FOR WEST AFRICA

## Manufa

Don bunkasa harkokin dimokuradiyya a Gwamnatin Najeriya ta hanyar tallafa wa al'umma su samu bayanai, su shiga harkokin gwamnati a dama da su, tare da hadin gwiwa da al'ummar mazabu da yankunan karkara da kungiyoyin fafutikar hakkin al'umma da hukumomin gwamnati.

**KUNGIYAR RIGHT TO KNOW…** *Rayuwarku ta dogara a kanta*

# ABUBUWA 10 DA ZA A FAHIMTA GAME DA DOKAR 'YANCIN SAMUN BAYANAI (FOIA) TA 2011

Daga

Ene Enonche[1]

Sabuwar Dokar 'Yancin Samun Bayanai (FOIA), wadda Shugaba Goodluck Jonathan ya rattaba wa hannu a ranar 28 ga watan Mayun 2011, ta kunshi muhimman tanade-tanade da za su sauya tsarin sirrinta harkokin gwamnati, wadanda a da al'adar hukumomin Gwamnatin Najeriya ne. Muhimmin abu game da dokar shi ne jami'an hukuma su aka danka wa amana a madadin dimbin al'umma da ke da hakkin su san abin da suka aikatawa. Abu mafi muhimmanci, shi ne Dokar 'Yancin Samun Bayanai ta (FOIA) ta yi niyyar kawar da rudanin da kebance jami'an hukuma kan yadda suka asirta harkokin gwamnati da hukumomi, tare da yadda ake killace bayanai. Wannan takaitaccen bayani ya fito da muhimman tande-tanade 10 da ke kunshe a Dokar 'Yancin Samun Bayanai (FOIA).

## 1. Dokar FOIA Tana Sama Da Dokar Boye Asirin Gwamnati (OSA)

Sashi na 1 (1) na dokar ya tanadi cewa: "Kowane mutum yana da hakkin samun bayanai, wadanda ke adane ko a rubuce da suke hannun jami'in gwamnati ko hukuma ko wata cibiya, kuma an yi bayani kanta." Wannan hakki tabbas "ba tare da la'akari da wata doka ko ka'ida ba." Wannan tanadi na nufin cewa dokar FOIA tana da fifiko a kan dokar asirta ayyuka. Sai dai Dokar 'Yancin Samun Bayanai (FOIA) ba ta da irin wannan tasiri kan Dokar Hukumomin Tsaron Kasa, saboda wannan dokar na kunshe ne a cikin kundin tsarin mulki, kuma akwai hanyoyi na musamman da sashi na 9 (2) na Kundin tsarin mulkin ya tsara don bi kafin a yi mata gyara kuma hakan bai shafe ta ba a wannan yanayi.

## 2. Kowa Zai Iya Neman Bayanai A Karkashin Dokar FOIA

Hakkin da dokar FOIA ta tanada hakkin kowa ne, ba tare da la'akari da bambancin shekaru ko kabila ko jinsi da makamantansu ba, kafin a ba mutum damar samun

[1] Ms. Enonche ita ce Shugabar Kungiyar Right to Know (R2K)

bayanai da ke karkashin kulawar hukumomin gwamnati da kamfanoni masu zaman kansu da ke gudanar da ayyukan ga al'umma a madadin gwamnati. Wannan doka ta tanadi cewa mutanen da ke da nakasa ko karancin ilimi za su iya samun bayanai; ta tanadi cewa irin wadannan mutane za su iya gabatar da bukatarsu ta hannun wakilansu. Abin sha'awa, shi ne dokar ta tanadi cewa babu wanda za a ce sai ya bayyana dalilinsa na neman bayanai ko kuma hakikanin abin da ya sa yake bukata.

### 3. Wajibi Ne A Bayar Da Bayanai Ga Mai Bukata Cikin Mako Daya

Sashi na 4 da na 5 na Dokar FOIA ya tanadi cewa hukumomin gwamnati su bayar da bayanan da ake bukata cikin kwanaki bakwai. Kuma an ba hukuma karin kwanaki uku da ake bukatar ta mika bayanai ga wata hukuma, idan ta gano cewa wata hukumar na da wadansu bayanai da ke karkashin kulawarta da ake nema. A kowane irin yanayi idan aka samu cewa bayanin da ake nema yana da yawa, doka ta tanadi karin wa'adin yini bakwai. Idan har akwai wani dalili da hukuma za ta ki bayar da bayanai, karkashin tanade-tanaden doka kamar yadda yake a rubuce, dole ne a sanar da mai nema, a kuma bayar da cikakken bayani da dalilan da suka sanya aka hana bayanan.

### 4. Akwai Hukunci Ga Wanda Ya Lalata Bayanai

Sashi na 10 da ke kunshe cikin dokar, ya yi gargadi kan lalatawa ko samar da bayanan karya. Lalata bayanai laifi ne a karkashin dokar, wanda hukuncinsa ya tanadi zaman kurkuku na shekara daya ga jami'i ko shugaban hukumar gwamnati, al'amarin da ke kunshe a sashi na 7(5) na dokar wanda ya tanadi tarar Naira dubu 500 da za a dora wa hukuma ko jami'in gwamnati wanda ya yi kuskuren kin bayar da bayanai.

### 5. Za A Iya Cin Tara A Matsayin Biyan Asarar Da Aka Yi Wajen Maimaita Kwafen Bayanai

Samun bayanai kyauta ne. Sai dai sashi na takwas na Dokar 'Yancin Samun Bayani (FOIA) ya tanadi cewa "cajin kudi an kayyade shi ga kimar bayanai da za a kwafa, ko a rubuta su, matukar bukata ta taso."

## 6. Dole Ne Hukumomin Gwamnati Su Adana Bayanai Yadda Ya Kamata

Dokar 'Yancin Samun Bayanai (FOIA) ta dora nauyi a kan hukumomin gwamnati su tabbatar da cewa sun tattara bayanai kan ayyukan da suke gudanarwa da aiwatarwa da hada-hadarsu. Sannan akwai bukatar su adana bayanan yadda ya kamata, don a samu saukion samun irin wadannan bayanan, tare da wallafa bayanai game da hukuma a jarida, ko yadawa a rediyo da talabijin da shafukan yanar sadarwar intanet. Haka kuma dokar ta tabbatar da cewa dole ne hukumomin gwamnati su horar da jami'ansu kan tanade-tanaden dokar da kuma yadda ya dace a aiwatar da dokar.

## 7. Za A Bayar Da Kariya Ga Masu Tonon Silili

Sashi na 27 na Dokar 'Yancin Samun Bayanai (FOIA) ya bayar da kariya ga jami'an gwamnati dangane da gurfanar da su a gaban shari'a saboda "bayar da bayanai da kyakkyawar niyya" bisa la'akari da Dokar 'Yancin Samun Bayanai (FOIA). Don haka jami'an gwamnati da suka tona asirin gazawar hukuma wajen aiwatar da aiki ko amfani da mukami ta hanyar da bai dace ba, da almubarrzanci da dukiyar al'umma ko cin hanci da rashawa, suna da kariyar shari'a da ta kange su daga gurfana gaban kotu ko yi musu bi-ta-da kulli.

## 8. Wadansu Rukunin Bayanan Da Aka Tsame Su Daga Bayanawa

Sashi na 11 zuwa 17 na dokar ya tsame wadansu rukunin bayanai daga bayyana ga jama'a. Irin wadannan bayanai da aka tsame sun hada da bayyana al'amuran da za su kawo illa ga harkokin kasashen waje da tsaron Najeriya ko bayanai kan harkokin mulki don tabbatar da doka da gudanar da bincike ko bayanan da suka shafi sirrin mutum na kashin kansa ko bayanan da suka shafi mutum na uku da suka hada da sirrin ciniki ko bayanan kasuwanci da hada-hadar kudi ko bayanan da suka shafi alfarmar kwwararru, da suka hada sirrin majiya a aikin jarida, ko lauya game da wanda yake karewa ko jami'in kiwon lafiya game da wanda yake wa jinya, da takardun kwas, wadannan tabbas an tsame su.

## 9. Akwai Hakkin Neman Bayani Ta Kai Kara Ciki Har Da Bukatar A Sake Duba Batun A Kotu

Dokar ta bayar da dama ga kowa ya kai kara kotu don tilasta kowace hukumar gwamnati ta yi aiki da tanade-tanaden dokar. Sannan ta kayyade wa'adin kwanaki 30 ga mutumin da wata hukumar gwamnati ta hana shi bayanai ya kai kara a gaban kotu don shari'a ta bi kadin lamarin. Hukumar Kare 'Yancin Dan Adam ta Kasa ma tana da muhimmiyar rawar da za ta taka a karkashin dokokin da suka shafe ta, don tabbatar an bayar da 'yanci da hakkokin da ke kunshe cikin Dokar 'Yancin Samun Bayanai (FOIA).

## 10. Ministan Shari'a Ke Da Alhakin Ganin Ana Aiwatar Da Dokar 'Yancin Samun Bayanai (FOIA) Yadda Ya Kamata

Matsayin dokar, shi ne ta dora babban nauyin aiwatar da tanade-tanadenta ga Ofishin Ministan Shari'a. A farkon watan Fabrairun kowace shekara daukacin Ma'aikatun Gwamnatin dole su gabatar wa Ministan Shari'a rahoton yawan bayanan da suka ki bayarwa tare da dalilansu na kin bayar da bayanan a inda bukatar hakan ta taso da kuma adadin masu bukatar bayanan da hukuncin kotu game da matsayin hukumomin na kin bayar da bayanai da kuma yawan kudin da suka karba don nazarin takardun bukatun da aka gabatar musu, sannan da yawan ma'aiaktan da aka dora wa alhakin bibiyar takardun bukatar bayanai.

## RUDANI 10 DA KE TATTARE DA DOKAR 'YANCIN SAMUN BAYANAI

Daga

Chidi Anselm Odinkalu[2]

Shugaba Goodluck Jonathan ya amince da Dokar 'Yancin Samun Bayanai (FOIA) a ranar 28 ga Mayun 2011. Da wannan mataki dokar ta fara aiki. Sai dai al'amuran da aka saba ji game da tarihi da asali da abin da dokar ta kunsa da yadda aka kafa ta da manufofin da take son cimmawa da sauran al'amuran da suka shafi dokar, suna ci gaba da kawo rudani. Don haka za mu yi kokarin warware rudanin.

## RUDANI NA 1: ANA GANIN DOKAR FOIA A MATSAYIN TA 'YAN JARIDA CE

Gaskiyar lamari: Dokar 'Yancin Samun Bayanai (FOIA) an tsara ta ne don ta samar da daidaito a tsakanin al'umma, wajen shiga a dama da su a harkokin gwamnati. Manufar dokar ita ce ta tabbatar da cewa kowane mutum da yake bukatar sanin yadda gwamnati ke gudanar da ayyukanta, za iya samun haka ba tare da wata wahala ba. Daidaikun mutane ko kamfanoni za su samu hakkokin da ke kunshe a cikin dokar. Akwai kwarin gwiwa, ganin cewa mutane za su iya motsawa don yi aiki tare da gwamnati, su bayyana matsayinsu, su kuma shirya yadda za su binciki jami'an gwamnati. Akwai tabbaci kan cewa dokar za ta inganta rahotannin kafafen yada labarai da gudanar da bincike, ta yadda za a shawo kan yada jita-jita, a kuma kyautata yadda ake tantance gaskiyar al'amura da ke tattare a cikin bayanai. Ba za a iya cin nasara ba, har sai jami'an gwamnati wadanda nauyin aiwatar da dokar ya rataya a kansu sun yi aiki da gaskiya da kwarewa. Su ma kamfanoni da 'yan kasuwa sai sun bi doka sau da kafa.

[2] Odinakalu Jigo ne a Kwamitin Gudanarwa na Kasa na Kungiyar Lauyoyin Najeriya (NBA), kuma yana aiki tare da Kungiyar Open Society Foundation (OSF).

## RUDANI NA 2: MAJALISAR DOKOKI TA KASA TA “SAUYA” TA KUMA “RAUNATA” DOKAR ʼYANCIN SAMUN BAYANAI (FOIA) KAFIN TA AMINCE

Gaskiyar lamari: Majalisar Tarayya ta amince da kudirin Dokar ʼYancin Samun Bayanai a ranar 24 ga Fabrairun 2011, ita kuwa Majalisar Dattijai ta amince da wani nau'i na daban na kudirin dokar a ranar 16 ga watan Maris 2011. Akwai bambance-bambance har goma sha biyu tsakanin kudurorin da Majalisar Dattijai da ta Wakilai suka amince da su. Wadannan bambance-bambance sun tabo muhimman al'amura na tsarin inda tunanin majalisun suka karkata. Kundin da Majalisar Dattijai ta yi aiki a kai ya tattaro manufar hakkin samun bayanai a wajen hukuma a matsayin alfarma; shi kuwa wanda Majalisar Tarayya ta yi aiki a kai ya tabbatar da kundin dokar a matsayin hakki ne. Kamar yadda aka bukata ga tsarin majalisa, kowace majalisa ta wakilta mutum shida don halartar taron kwamitin daidaita mabambantan kudirorin dokar. Wannan shi ne kundi na karshe da daukacin majalisun suka amince da shi a ranar 24 ga watan Mayun, 2011. Sakamakon hakan, duk wadansu bambance-bambance da ke tsakanin wadancan kudirori biyu, an warware su, an daidaita su don fitar da kwakkwarar doka. Sabanin yadda ake ta yadawa, Dokar da Shugaban Kasa ya rattaba hannu a kai ta fi nagarta a kan mabambantan dokokin da daidaikun majalisun suka amince da su a baya.

## RUDANI NA 3: DOKAR ʼYANCIN SAMUN BAYANAI DOKAR ABIKE DABIRI CE

Gaskiyar lamari: Dokar Samun ʼYancin Bayanai ta Najeriya, an samar da ita ce ta hanyar hadin gwiwa tsakanin al'ummar kasa da kungiyoyin fafutikar kare hakkin al'umma da gwamnati. An shafe shekara 17 tun sa'adda aka fitar da kudirin dokar zuwa ranar da aka fara aiki da ita. Kudirin Dokar ʼYancin Samun Bayanai ta samo asali ne daga Edetaen Ojo, Babban Daraktan Kungiyar Kare Hakkin Kafafen Yada Labarai ta MRA, tare da taimakon Kungiyar ʼYan jarida ta Najeriya (NUJ) da kungiyoyin Fafutikar Hakkin Al'umma (CLO). Tsarin farko na kudirin dokar, an shirya shi ne a 1994, wanda kuma ya tsara shi ne Tunde Fagbohunlu, wanda a yanzu Babban Lauyan Najeriya ne (SAN), kuma abokin hadin gwiwarsa Aluko & Oyebode, shi ma Babban Lauyan Najeriya (SAN), sun samu taimakon Marigayi Bankole Aluko (wanda ya zama Babban Lauyan Najeriya -SAN daga bisani) da Chidi Anselm Odinkalu. ʼYar Majalisa Abike Dabiri-Erewa tana cikin manyan magoya bayan kudirin da aka gabatar a gaban Majalisar ta biyar, kuma tana daya daga cikin wadanda suka dauki nauyin kudirin a karshen wancan majalisar, tare da Ita Enang

da Dino Melaye. Baya ga haka ma a lokacin da aka fara gabatar da kudirin ba ta ma shiga majalisar ba, wato a cikin watan Yunin 1999. Tarihi ya tabbatar da cewa yayin da aka gabatar da kudirin a Majalisar Tarayya a 1999, wadanda suka gabatar sun hada da marigayi Tony Anyanwu da Nduka Irabor da Jerry Ugokwe.

## RUDANI NA 4: DOKAR 'YANCIN SAMUN BAYANAI BARAZANA CE GA TSARON KASA

Gaskiyar lamari: Tsaron Najeriya hakki ne da ya rataya kan kowa da ke zaune a cikinta, ko kuma ya fito daga cikinta. Sabanin yadda ake zargin za a yi wa harkar tsaron kasa illa, Dokar 'Yancin Samun Bayanai (FOIA) za ta tallafa wa masu ruwa da tsaki a Najeriya, za ta kauce wa bayyana wadansu kebabbun al'amura, haka kuma ta tanadi kariya ga masu tonon silili a sashe na 27. Dokar 'Yancin Samun Bayanai (FOIA) na kunshe da tanade-tanade da suka kebe wadansu al'amura a sashi na 11 zuwa 19 da na 26. Bayanai da aka kebe daga bayyanawa a karkashin dokar da ke sashi na 11 (1) "duk wani bayanin da idan an bayyana shi zai bata kimar kasar nan a idon kasashen duniya ko illa ga harkokin tsaron Tarayyar Jamhuriyya Najeriya," haka kuma a karkashin sashi na 12 (1), bayanan da za su kawo cikas wajen gudanar da binciken miyagun laifuffuka da kuma tabbatar da bin doka. Wannan ya shafi 'yan sanda kurum. Wadannan tanade-tanade suna karfafa Dokar Hukumomin Tsaron Kasa ta 1986, wadda ke kunshe a a sashi na 315 (5) (c) na Kundin Tsarin Mulkin 1999, wadda za a iya yi mata gyaran fuska ne kawai ta hanyar tanade-tanade na musamman da ke kunshe a karkashin sashe na 9 (2) na kundin tsarin mulkin. Dokar Hukumomin Tsaron Kasa, ta kafa hukumomi uku da aka dora wa nauyi na musamman, don bayar da kariya da tabbatar da tsaron Najeriya. Wadannan hukumomi su ne:

(a) Hukumar Leken Asiri ta Soja (DIA), don ayyukan tsaro da kula da harkokin soja.
(b) Hukumar Leken Asiri ta Qasa (NIA), don tsaron martabar Najeriya a kasashen waje; da
(c) Hukumar Tsaron Cikin Gida (SSS), don bayar da kariya ga tsaron cikin gida a Najeriya.

An samar da Mai Bayar da Shawara kan Harkokin Tsaro na Kasa (NSA) a karkashin sashi na 4 na wannan doka a matsayin mai "gudanar da harkokin tsaron kasa." Kuma sashi na 2 (3) (a) na Dokar Hukumomin Tsaron Kasa ya tanadi cewa Jami'an

Tsaron Qasa na SSS su tabbatar da “tsaron al’amuran da suka shafi farar hula wadanda ke da alaka da tsaron cikin Najeriya.” Sannan kuma, wadannan tanade-tanaden na Dokar Hukumomin Tsaron Kasa za su ci gaba da zama kebantattun bayanai, musamman game da bayanan da aka kebance su a matsayin masu matukar barazana ga harkar tsaron kasa.

## RUDANI NA 5: MUNA BUKATAR DOKAR BOYE SIRRIN GWAMNATI

Gaskiyar lamari: Dokar Boye Sirrin Gwamnati da ake amfani da ita a Najeriya, an samo ta ne daga gwamnatin mulkin mallaka ta Birtaniya a 1911, sannan aka shigo da ita Najeriya a matsayin dokar mulkin mallak bayan an hade kasar. Gwamnatin mulkin mallaka ta Birtaniya ba ta da al’ummar kasa; sai dai talakawa a karkashinta. Kwatankwancin wannan, a karkashin mulkin mallaka akwai ’yan kasa. A karshen mulkin mallaka, Najeriya ta zauna a karkashin mulkin soja, kuma tsawon zamanin mulkin soja al’ummar kasa ba su cika sanin halin da ake ciki ba. A karkashin mulkin farar hula, wanda aka gina karkashin amincewar masu kada kuri’a, Dokar ’Yancin Samun Bayanai (FOIA) wata hanyar ce ta tabbatar cewa al’ummar kasa za su iya samun bayanai kan halin da wakilan da suka zaba da hukumomi ke ciki. Wannan zai ba su dama su yanke wa kansu hukunci, kan su ci gaba da tafiya tare da su ko su yi musu garambawul ko kuma su sauya su. A Birtaniya inda dokar sirrin ta samo asali, ana yawan yi mata gyaran fuska daga lokaci zuwa lokaci. Yanzu aikinta kacokan ya ta’allaka ne ga jami’an tsaro da tattara bayanan sirri. Idan an kwatanta zamanin mulkin mallaka dokar sirrin aikin hukuma ba a taba yi mata gyaran fuska a Najeriya ba, har zuwa yau.

## RUDANI NA 6: BA ZA A IYA AIKI DA DOKAR ’YANCIN SAMUN BAYANAI (FOIA) A JIHOHI BA

Gaskiyar lamari: Dokar ’Yancin Samun Bayanai (FOIA) na tafiya a mabambanta dokokin tsarin mulki biyu cikin kebantaccen ikon Majalisar Dokoki ta Qasa. Na farko a karkashin sakin layi na 3 (c) na Rataye na 3, inda Kundin Tsarin Mulki ya ba Majalisar Dokoki ta Kasa ikon bayar da sharuddan samun bayanai kan bayyana kadara ga ma’aikatan hukuma. Na biyu, a bayani na 60 (a) da aka fitar a Rataye na 2, da ya shafi karfin ikon Majalisar Dokoki wajen samar da dokoki da tabbatar da ana aiki da muhimman manufofi da umarnin tsare-tsaren kasa da ke kunshe a Babi na biyu na Kundin Tsarin Mulki. Sashi na 14 (2) (a) na Kundin Tsarin Mulki, a

wannan babi ya tabbatar da cewa “Iko na al’ummar Nijeriya ne wadanda daga gare su gwamnati ke samo ikonta,” yayin da sashi 14 (2) (c) ya tanadi cewa “a tabbatar an ba mutane damar shiga a dama da su a cikin harkokin gwamnati…” Dokar ’Yancin Samun Bayanai (FOIA) tana sauke waxannan nauyi na Majalisar Dokoki ta Kasa. Dadi a kan haka, abin da ke karkashin bayani na C. 4 a kashi biyu na Rataye na 2 na tsarin mulki ya fitar da jerin ayyukan majalisar cewa “Majalisar Dokoki ta Kasa za ta iya samar da dokokin ga Tarayya ko wani yanki da ke cikinta, tare da la’akari da kundin bayanan Tarayya.” Ba wai an hana jihohi tsara dokoki ba ne, amma irin wadannan dokoki, suna kasa da Dokokin Tarayya, musamman idan akwai matsalar da za ta kawo cikas ga hakkokin da ke cikin dokar tarayya. Idan ba a samu irin wadannan dokokin jiha ba, to Dokar ’Yancin Samun Bayanai (FOIA) za ta yi aiki a jihohi.

## RUDANI NA 7: DOKAR ’YANCIN SAMUN BAYANAI (FOIA) ZA TA HAIFAR DA KETA HADDIN SIRRI DA BA ZA A AMINCE DA SHI BA

Gaskiyar lamari: Sashi na 14 na Dokar ’Yancin Samun Bayanai (FOIA) ya tanadi cewa: “Hukuma dole ta ki amincewa da bukatar neman bayanan da suka shafi sirrin kashin kai na wani,” sannan an yi cikakken bayani kan jerin al’amuran da za su iya zama bayanan sirrin kashin kan wani. Sai dai bisa la’akari ake gudanar da harkar neman bayanai a kasashen duniya, kebe bayanai zai iya yiwuwa ne bisa la’akari da bukatar al’umma. Kari a kan haka, dokar ta tanadi kariya daga bayyanawa a sashi na 16, game da bayanan da suka shafi lauya ko wanda yake bai wa kariya; jami’in kula da lafiya ko mara lafiya ko sirrin majiyar aikin jarida.

## RUDANI NA 8: DOKAR ’YANCIN SAMUN BAYANAI (FOIA) ZA TA BUDE KAFAR TSAGERANCIN KAFAFEN YADA LABARAI

Gaskiyar lamari: Maimakon bude kafar tsagerancin kafafen yada labarai, Dokar ’Yancin Samun Bayanai (FOIA) an tsarata ne yadda za ta kange aukuwar hakan. A gwamnatocin baya, inda aka kebance samun bayanai ga ’yan tsirarun masu rike da mukaman gwamnati, don haka ake samun uzirin nuna gazawa wajen aiwatar da aikin jarida, al’amarin da kan haifar da yada jita-jita. Don haka Dokar ’Yancin Samu Bayanai (FOIA), tare da kafafen yada labarai da sauran masu bukatar tattarawa da bugawa ko wallafa kundin bayanai, za su iyi aiki tukuru wajen tantance ingancin bayanan. Cikin sauki, suna da nauyin da za su sauke bisa irin kwarewarsu wajen

bayyana irin kokarin da suka yi na samowa da tantance bayanai. Alal misali akwai yiwuwar, yayin da ake tafka shari'a kan keta haddi ko cin zarafi, kotu na iya yin la'akari da gazawa da rashin yin kokari wajen tattara bayanai, gyare-gyare da bayar da hakkokin da kotu ta bayar. A duniyar wallafe-wallafe, Dokar 'Yancin Samun Bayanai za ta saukaka kashe kudi wajen tattara labarai, sannan an bude kafar yada labaran gaskiya a kafafen yada labarai.

## RUDANI NA 9: BABU HUKUMAR DA ZA TA AIWATAR D ADOKAR 'YANCIN SAMUN BAYANAI (FOIA)

Gaskiyar lamari: Dokar 'Yancin Samun Bayanai (FOIA) ta shafi kowace ma'aikata da hukumomin gwamnati, har ma da kamfanonin masu zaman kansu da suke gudanar da aikace-aikace ga gwamnati , ko suke sarrafa dukiyar gwamnati." Ma'anar wannan rukunin, akwai tabbacin cewa za a tabbatar da shi a aikace da hukunce-hukuncen dokokin shari'a. Kowace hukuma da dokar ta shafa za ta mika rahoton shekara-shekara ga ofishin Ministan Shari'a, wanda ke da karfin ikon bibiyar dokar, ya kuma kai rahoto ga Majalisar Dokoki ta Kasa a kowace shekara kan yadda ake aiwatar da dokar. Dokar ta bayar da karfin iko ga hukumar bibiya da nazarin shari'a a kotuna. An jajirce kan cewa Hukumar Kula Da 'Yancin Dan Adam ta Kasa ke da hakkin tabbatar da hakkokin da dokar ta tanada.

## RUDANI NA 10: BA MU SHIRYA WA DOKAR 'YANCIN SAMUN BAYANAI (FOIA) BA

Gaskiyar lamari: Al'ummar kasa da suka shirya zaben wakilansu, su tura su Abuja ko Hedkwatar Jiha ko Karamar Hukuma, don tafiyar da harkokin al'umma, tabbas dole a tabbatar da suna cikin cikakken shirin son su san ayyukan da wakilansu da hukumomin gwamnati ke a yayin da suka kai inda aka tura su.

Contact:
Plot 3685 Erie Close,
Off Erie Crescent, Off Nile Street
Maitama, Abuja- Nigeria
Tel: +234 9 7802227
info@r2knigeria.org
www.r2knigeria.org